Babu wasu musulmai biyu da zasu haɗu sannan su gaisa hannu da hannu sai an gafarta musu kafin su rabu

Daga Bara'u - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce -: "Babu wasu musulmai biyu da zasu haɗu sannan su gaisa hannu da hannu sai an gafarta musu kafin su rabu".
[Ingantacce ne a baki dayan hanyoyin sa] [Abu Dawud da Tirmizi da Ibnu Majah da Ahmad ne Suka Rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya bada labari: Cewa babu wasu musulmai biyu da zasu haɗu a wata hanya da makamancinta ɗayansu ya yi wa ɗayan sallama, gaisuwa hannu da hannu sai an gafarta musu kafin su rabu da jikkuna ko da gama gaisuwar.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/6257